# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Cin zarafi ta hanyar lalata tsakanin al'umma a Afirka
## Kashi na tara: Babu wani dalili

| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |

**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Fati: | 'yar shekara 16 |
| Sherifat: | 'yar shekara 40 |
| Mai karanta labarai: | ɗan shekara 25 |
| Julie: | 'yar shekara 40 |
| Precious: | 'yar shekara 30 |
| Adams: | ɗan shekara 10 |

**Mai gabatarwa:**

Masu sauraronmu, barkanmu da sake kasancewa da ku a cikin wannan shiri na “Ji Ka Karu” wanda shi ne kashi na tara a kan cin zarafin ’ya’ya mata. A cikin shirin da ya gabata kun ji yadda mai fafutukar yaƙi da cin zarafin matan nan, wato Julie, ta ƙwaci Fati daga hannun malaminta Malam Tanko wanda saura ƙadan ya ci mutuncin ’yar ƙaramar yarinyar. Daga baya kuma an tilasta wa Malam Tanko ajiye aikinshi na malamanta a makarantar. Yanzu Julie na ƙoƙarin shirya wani taro ne da nufin shawo kan ’yan majalisa su tsaurara dokar cin zarafi da fyaɗe. Tana buƙatar waɗanda aka ci zarafinsu kuma suke samun shawarwari a cibiyarta da su bayyana wa duniya halin da suka shiga. Abin mamaki, sai Hadiza ta yarda za ta fito fili ta faɗi labarinta. A halin da ake ciki kuma an ɗaure Kawu Jammo na tsawon shekaru biyar saboda cin zarafin ɗan matar nan da yake nema, wato Adams wanda shekarunsa goma ne kacal. A yanzu Adams na ƙoƙarin neman waraka daga abin da ya same shi duk da cewa hakan yana zuwa da ’yar wahala.

Taken shirin na yau shi ne “Babu dalili”, kuma za a faro ne daga gidan su Fati inda take hira da mahaifiyarta Sherifat a ƙarshen mako.

**Fitowa ta 1: A gidan su Fati**

**Fati:** Sannu Mama!

**Sherifat:** Yauwa sannu Fatina. Na ji daɗi yadda kika koma kamar da. To yaya wasannin motsa jikin?

**Fati:** Lafiya lau. Ina ganin na fara…

**Sherifat:** Fati, na ji daɗin yadda kika fito kika yi min bayani a kan Malam Tanko. Ban taɓa tsammanin cewa zai yi irin abin da ya yi ba! Irin waɗannan mutane bai kamata a ce an kulle su ne kawai ba, kamata ya yi a ce an yi musu hukunci mai zafi!

**Fati:** Mama!

**Sherifat:** Ki yi haƙuri Fati! Ɓa na iya jure tunanin abin da ya yi miki, irin cin zarafin da ya yi miki. Abin yana ɓata min rai sosai, kuma abin yana damuna sosai da na kasa taimakonki.

**Fati:** Haba Mama, ki bar maganar nan haka. Ina ƙoƙarin in manta da abin da ya faru. Julie ta riga ta ba da rahoto a wurin yan sanda, kuma suna ɗaukar mataki a kan al'amarin, kuma tana taimaka min don in manta da al'amari. Yauwa, na ma tuna da maganar Julie. An jima zan je cibiyarta. Na faɗa miki cewa tana shirya wani taro?

**Sherifat:** A'a! Wane irin taro ne?

**Fati:** Tana so ne waɗanda aka ci zarafinsu ko aka yi musu fyaɗe su fito su faɗi labarinsu kowa yana ji. Tana tunanin cewa yin hakan zai iya sa gwamnati ta ƙara canza dokar da ake da ita a kan cin zarafi. Ta ce ya kamata a ce hukuncin da ake yi mai zafi ne in har ana so ya zama ishara ga wasu.

**Sherifat:** Amma in ce dai ba ta ce miki ki faɗi naki al'marin ba ko? Ina ganin bai kamata mu faɗa wa mutane da yawa wannan maganar ba.

**Fati:** A'a, ba ta tambaye ni kai tsaye ba. Amma dai ta tambayi wanda zai yi hakan don kanshi. Kuma ina ganin mace ɗaya ce kawai ta amince.

**Sherifat:** Fati, ki yi hakuri kin ji 'yata, ganin cewa ban lura da alamomin ba, wataƙila duk da abin bai kai ga haka ba. Da na gane cewa abubuwa ba sa tafiya daidai. Yanzu faɗa

min, yaya kike ji yanzu bayan duk abubuwan da suka faru? Yaya ki ke ji?

**Fati:** Mama ni ƙoƙari nake in manta da komai. Ni fatana ke nan. Ina so ne in ci gaba da rayuwata ba tare da na ƙara tunanin abin da ya faru ba.

**Sherifat:** Hmm… Na gane Fati, na yi alkawarin yin duk abubuwan da ya kamata don in taimaka miki. Yanzu sai ki je ki cire waɗannan kayan masu zufa daga jikinki.

**Fati:** To Mama, na ji, Ko za ki ɗan kunna mana rediyon nan, mu ji waƙa mai kwantar da hankali? Yanzun nan zan dawo.

**Mai karanta labarai:** Kuma wannan duk a cikin labaran: Kungiyar yaƙi da cin zarafin mata za ta gudanar da wani babban taro a ƙarshen makon nan. Taron zai gudana ne a lokacin da hali na cin zarafin mata da fyaɗe yake ta ƙaruwa. Masu shirya taron sun ce manufar taron ita ce don a fito da ainihin gaskiyar yadda wannan matsala take aukuwa, wanda ake ganin ya shafi kashi 25 na yawan al'umma. Kuma suna da niyyar nuna irin wahalhalu da matsalolin da waɗanda aka ci zarafinsu…

**Sherifat:** A'a'a , kai! Ko me yake faruwa ne a ƙasar nan tamu? Wa ya kamata a zarga a kan wannan abin? Kai, ta ina kuma muka yi laifi?

**Fati:** Mama, na dawo… wai ba wani abin kirki ne da za a ji a rediyon nan?

**Sherifat:** A'a! Kin san wani abu ne, Fati? Ina ganin ya kamata ki shirya ki je wurin Julie. Ni da kaina ma zan raka ki.

**Fati:** Mama lafiya dai? Kamar kina cikin damuwa!

**Sherifat:** Ai ina ganin haka ne. Ban yarda da irin abubuwan da nake ji ba. Ke dai, shirya mu tafi Fati.

**Mai ba da labari:**

Ba Sherifat kaɗai ce ke irin waɗannan tambayoyin ba. Mutane da yawa na mamakin abin da ya sa cin zarafin mata da fyaɗe ya yi yawa a yawancin ƙasashen nahiyar Afirka. Shin wannan abin al'ada ce? Wataƙila, saboda a ƙasashen Afirka maza na da iko sosai ne a kan mata. Har yanzu hankalin Sherifat bai yarda da cewa wai malamin 'yarta, wato Tanko, shi ne ya yi ta cin zarafin ta 'yarta ba. Amma bayan ta saurari wannan labarin a rediyo, sai ta yanke shawarar ta bi Fati don ta kai wa ƙungiyar Julie ziyara.

**Fitowa ta 2: A cibiyar Julie**

**Julie:** Shi ke nan, shi ke nan. Kowa ya shirya wa taron? … To, ya yi daidai. Yanzu ina yi wa kowa sannu da zuwa. … To, don Allah kowaccenku sai ta tunawa 'yar'uwarta abin da ya kamata ta yi idan ta samu kanta a cikin mawuyacin hali na barazana.

**Sherifat:** Sannu Malama, sunana Sherifat. Ni ce mahaifiyar Fati. Ba na zo ba ne a kan dalilan da suka kawo ku nan, na rako 'yata ce kawai. Amma ina so ne in ce ban taɓa tsammanin cewar cin zarafin da ake yi wa mata a ƙasar nan tamu ya yi yawa haka ba.

**Julie:** A gaskiya ma wanda muka sani kaɗan ne a kan wanda ba mu sani ba. Akwai jama'a da yawa da suka samu kansu a

cikin wannan hali amma ba su fito fili sun faɗa ba. Ko kin san cewa, misali a Afirka ta Kudu ana yi wa mata fiye da ɗari da hamsin fyaɗe a rana?

**Sherifat:** Mene?! Wannan bai yiwuwa. Ta yaya mata ke iya rayuwa a irin wannan ƙasar?

**Judie:** Kin yi tambaya mai kyau. Amma ba ita ce ƙasa kaɗai ba da ake fama da matsaloli na cin zarafin da ya fi shafan mata ba. A gabashin ƙasar Congo, an nuna cewa matsalar cin zarafi da wulaƙanta mata ya fi yawa a ko'ina a duniya. An ƙiyasta cewa akwai fiye da mutane dubu ɗari biyu da aka yi musu fyade a Jamhuriyyar Congo.

**Sherifat:** Bai yiwuwa! Mutane dubu ɗari biyu da aka yi musu fyade?! Sannan shi ne nake zaune a nan nake tunanin cewa Fati na ɗaya daga cikin kaɗan. Ki yi haƙuri na ɓata miki lokaci, na zo nan da Fati ne kawai saboda ina…

**Julie:** Saboda kina tunanin cewar wani abu zai iya faruwa da ita? Ko kuma zai faru da ke? Na sani. Dukkanmu muna da wannan tsoron. Tambayar ita ce, me za mu iya yi a kan matsalar?

**Sherifat:** Ban sani ba. Ni dai ina buƙatar 'yata ta girma ne a wurin da ba shi da hatsari kuma tana da kariya. Ni abin da zan iya tunani a kai ke nan kawai.

**Julie:** To ki zo mu yi taron da ke! Muna buƙatar taimakon kowa da kowa. Wannan yaƙi ne da ya kamata a yi tare. Yaƙi ne da zai iya samar mana da yanayi mai kyau kuma tsarkakakke. Yaƙi ne da kowa ya kamata ya yi.

**Mai ba da labari:**

Daga nan sai Julie ta ci gaba da bayanin irin muhimmancin da yake tattare da a miƙe tsaye don a yaƙi matsaloli na cin zarafi. Mutanen da suka ƙwaci kansu daga hali na cin zarafi na buƙatar taimako ne daga waɗanda suka yarda da su don su shawo kan damuwar da suka samu kansu a ciki, kuma su ƙara ci gaba da cuɗanya da ƙawaye da abokai.

A halin da ake ciki kuma, Precious na dafa wa Adams abincin da daddare. Shi ma Adams ya fara zuwa wajen Julie don samun shawarwari. Yanzun nan ya kammala wani rubutu da ya yi alkawarin yi mata kuma yana zaune ne yana jin waƙa a rediyo.

**Fitowa ta 3: A gidan su Adams**

**Mai karanta labarai:** Masu sauraro, barkanmu da sake saduwa. A wani rahoto da muka samu, an kama gogaggen ɗan ta'addan nan mai suna Shusha wanda ake zargin ƙungiyarsa ta 'yan ta'adda da aikata yin fyaɗe, musguna wa mutane, da wasu nau'o'i na cin zarafin mutane. Har ila yau, kotun hukunta masu aikata laifin cin zarafin mutane ta duniya na neman shi wannan mutumin, kuma za a gurfanar da shi a gabanta…

**Adams:** Mama! Mama! Yanzu aka kama 'yan ta'addan! Yanzun nan aka faɗa a rediyo.

**Precious:** Kai! Ai kuwa wannan labari ne mai daɗi, ɗana! Yanzu ka ga duk mutanen da suke zaune kusa da *border*, musamman mata, hankalinsu zai kwanta tun da ba za su ƙara fargabar cewa za a kai musu hari ba. To zo ka ci abinci. Sannan sai ka shirya ka je wurin Julie. Ka gama rubuta abin da ta ce ka rubuta?

**Adams:** E, na gama.

**Precious:** Kai ɗana, ina alfahari da kai sosai.

**Adams:** Mama, har yanzu ciwon cikina za dame ni.

**Precious:** Na sani, ɗana. Likita ya ce za a ɗauki ɗan lokaci kafin zafin ya daina. Za ka daina jin ciwon kwanan nan, kar ka damu ka ji?! To, zo mu ci abincin. Na dafa maka abincin nan da kake so ne! Sannan da zaran mun gama sai mu tafi cibiyar Julie don ka gan ta, idan ba haka ba dare zai yi mana. Ka ji?

**Adams:** To, Mama.

**Precious:** Yauwa!

**Mai gabatarwa:**
Da haka kuma muka kamala shirin na yau, sai a kasance da mu a shiri na gaba domin jin ko Julie za ta yi nasarar shawo kan gwamnati ta ƙara tsaurara dokokin cin zarafin mutane? Sannan shin Hadiza za ta iya fitowa ta ba da labarin abin da ya shafe ta na fyaden da aka yi mata? A kasance da mu a shiri na gaba don jin waɗannan. Kafin wannan lokaci kuna iya ziyartar adireshinmu na yanar gizo a dw.de/lbe, ko kuma adireshinmu na Facebook. Ku huta lafiya.